# Takardar Tsarin Aiki

Wannan takardar na da amfani wajen tsara ayyukanku. Da farko, ku fifita ayyukan da kuke son gudanarwa. Daga nan wannan takardar aiki za ta taimaka muku wajen tantance abubuwa game da aikin kamar su "wa?, me?, a ina?, yaushe?, da me ya sa?" sannan ku bi matakan tantance matsalolin da wata ƙila za a iya samu ko alʼamura ko ƙalubalen da za ku iya fuskanta yayin da kuke gudanar da aikinku. Wannan Matakin Gudanarwa zai nazarci haɗari da za a iya fuskanta da kuma matakan magance haɗari.

| TAKARDAR TSARIN AIKI |
|---|
| **ME: Taken Shiri, Taken Aiki, da kuma Manufar da ta Dace da Shirin** |
| **WA: Mahalarta/Masu Moriya da Abin ya Shafa (a sanya dukkan bayanan da suka samu, lambobin mahalarta, ƙasashensu, da sauransu)** |
| **TA YAYA:**<br>**Hanyoyi:**<br><br>Kayan Aikin da Ake Buƙata: |
| A INA: |
| YAUSHE: Yaushe ne za a gudanar a aikin, shin akwai abin da ya kamata ku lura da shi game da lokaci (misali, hutun addinai da na kasa daban-daban, lokutan da ake da su a rana, da sauransu) |

| ABUBUWAN DA YA KAMATA A LURA DA SU | |
|---|---|
| WHAT: Project Title, Activity Title, and Relevant Project Objective | |
| **HAƊURRA DA KA IYA AUKUWA** | |
| Haɗari | Tsarin Gudanarwa |

## Takardar Bayanai: Misalin Shirin P/CVE

**Hedayah danSearch for Common Ground sun samar da jerin ayyukan P/CVE daban-daban a cikin manhajarsu ta horaswa: Kokarin Shawo Kan Tsattsauran Ra'ayi: Gabatarwa ga Jagoranci Game da Batutuwa, Shirye-Shirye, da Tsarin Gudanarwa da ya Kamata. Kunshiyar batu, VE da daddale al'amarin rikici, ra'in shiri da kuma ƙarfin kungiyarku su ne abin la'akari yayin tsara ayyukan P/CVE. Duk da haka, wannan ya kasance jerin ayyukan P/CVE daban-daban ne domin su ba ku haske game da abubuwan da waɗansu ƙungiyoyi suka gudanar a wannan fanni.**

## WURAREN AIKIN P/CVE

### KARIYA NA BAI-ƊAYA

- Shirya tattaunawa tsakanin ƙabilu mabambanta domin gusar da kyamar al'adun waɗansu da gano al'amuran da ya dace a samu haɗin kai a kansu a cikin al'umma, musamman game da al'amuran da su ke kawo rabuwar kai a cikin al'umma wanda hakan ke haifar da tarzoma sakamakon tsattsauran ra'ayi.
- Ba da horaswa ga ma'aikatan jarida game da yadda za su bi matakan ƙwarewa domin rufe al'amuran da suka shafi tashin hankali domin guje wa ruruwar tashin hankali, da bakanta waɗansu al'ummu, ko kuma ƙara samun rarrabuwar kawuna.
- Kara koyar da dabarun kwantar da tarzoma ga shuwagabannin al'umma domin shawon kan ƙananan tashe-tashen hankula da samun matsaya game da matsaloli tare kuma da samar da haɗin guiwa domin shawo kansu a wuraren da tashe-tashen hankula suka kasance su ke jawo husumar masu tsattsauran ra'ayi.
- Nazartar matsalolin da tsattsauran ra'ayi ya samar game da wani al'amari takamaimai da kuma ɓangarorin da ke cikin haɗari tare da matuƙar buƙatar a yi hubbasa domin shawo kan matsalar tsattsauran ra'ayi.
- Taimaka wa shuwagabannin addinai domin shawo kan yadda masu tsattsauran ra'ayi ko fassara addini ta hanyar tsaurarawa, wanda yin hakan zai samar da sauki da fahimtar juna, sannan a shawo kan al'amuran da ke faruwa a wuraren da ake amfani da addini domin cusa wa mutane tsattsauran ra'ayi.
- Inganta matakan shawo kan tsattsauran ra'ayi a matakin gwamnati, matakan tsaro, al'umma, da kuma a sauran matakai ta hanyar tallafawa da gina al'umma.
- Inganta damar da ake da ita ta samun adalci, taimako ta fuskar doka, da kuma ingancin tsarin doka a cikin al'ummu yayin da al'amuran suka kasance su ke jawo tsattsauran ra'ayi.
- Karfafa matasa domin samun juriya ta hanyar amfani da bin matakan ilimi da suka shafi fahimtar kai da zurfafa tunani da kuma ilimin na'urorin zamani, yayin da aka fahimci cewa waɗannan al'amura na iya haifar da tsattsauran ra'ayi.
- Faɗakarwa da kara samar da matakan shawo kan matsalar tsattsauran ra'ayi a makarantu ta hanyar tattaunawa da matasa, malamai, farfesoshi, da manyan makarantu.
- Gina zamantakewa mai nagarta tare da yarda da mutunta juna tsakanin 'yan sanda da al'umma yayin da aka fahimci cewa yanayin zamantakewa ne ke harfar da tsattsauran ra'ayi.

## KEƁANTACCEN KARIYA

- Samar da haɗin kai ta hanyar dama wa da rukunen al'umma marasa rinjaye idan ya kasance waɗannan rukunen al'umma na iya zamowa masu tsattsauran ra'ayi yayin da ba a damawa da su.
- Samar da ilimin intanet da na kafafen sadarwa ga matasan da ke cikin haɗari domin su kasance masu kauce wa kiraye-kiraye da ka iya jefa su sahun masu tsattsauran ra'ayi game da rayuwar yau da kullum, matsayi, addini, da kuma al'amuran da suka shafi zamantakewa da siyasa.
- Faɗakar da mutanen da ke cikin haɗari ta hanyar taimaka musu domin su iya manyewa da damuwowi, su iya kwantar da hankalinsu, su iya kauce wa tsattsauran ra'ayi da rinjayuwa zuwa ga ra'ayoyin abokai, sannan su iya shawo kan matsaloli cikin lumana.
- Amfani da wasanni, fasahohi, da sauran matakai domin gina zamantakewa tsakanin matasan da ke cikin ƙalubale sannan a gudanar da tarurrukan ilimi domin gabatar musu da bayyanannun misalai game da al'amuranda da suka shafi zamantakewa ko siyasa.
- Taimaka wa matasan da abin ka iya shafi domin su fahimci musabbabi, alamomi, da matsalolin tsattsauran ra'ayi da kuma yadda mutane za su iya kauce wa wannan hanyar rayuwa, wanda za yi hakan ne ta amfani da bidiyoyin jawaban nadama daga masu tsattsauran ra'ayi a da.
- Samar da ƙungiyar matasa da jagororin matasa da suke shirye da su shawo kan matsalar tsattsauran ra'ayi tare da zama abin koyi ga matasa da matsalar tsattsauran ra'ayi ka iya shafa.
- Haɗa kai da fitattun mutane a cikin al'ummar da al'amarin ka iya shafa ko waɗanda a da suka kasance masu tsattsauran ra'ayi, domin magance tsattsauran ra'ayi a cikin al'umma ta hanyar ƙarfafa tattaunawa tsakanin mutanen da abin ka iya shafa tare kuma da samar da shirye-shiryen da ka iya samar da kariya daga matsalar.
- Ɗaukar matakan da za su sanya iyaye maza da mata da aka kai gidan kaso waɗanda suka nuna tsattsauran ra'ayi (waɗanda ke nan 'ya'yansu za su iya daukar halayensu) su riƙi kyawawan halaye, sannan a samar da darrusan koyar da reno da tarbiyantarwa domin kada iyayen su cusa wa 'ya'yansu tsattsauran ra'ayi.

## SA HANNU/KAUTARWA DA WURI

- Samar da lambar tuntuba ta gaggawa ga iyaye da sauran al'umma waɗanda ke da damuwar zargin wani da kasancewa mai tsattsauran ra'ayi.
- Kara faɗakar da 'yan sanda da jami'an gidan yari wajen gane alamomin tsattsauran ra'ayi tun yana kaɗan, wanda za a yi hakan ne ta hanyar inganta ƙwarwarsu a fannin bincike.
- Naɗa a na'ura da kuma gabatar da bayanan da za su iya sauya ra'ayoyin mutane wanda ya fito daga bakin waɗanda suka kasance masu tsattsauran ra'ayi ko waɗanda matsalar tsattsauran ra'ayi ta yi wa illa, domin ƙaryata farfagandar tsattsauran ra'ayi da ake yi wa mutanen da abin ya shafa.
- Samar da matakan da za su samar da jagoranci da tallafi ga malaman da ke cin karo da tsattsauran ra'ayi a azuzuwa.
- Ɗaukar mataki game da tsattsauran ra'ayi tun al'amarin yana ƙarami ta hanyar haɗa kai da ma'aikata da matasan ma'aikata da jami'an lafiyar ƙwakwalwa da kuma 'yan sanda.
- Mayar da hankali kan wadanda ke binciken rubuce-rubucen masu tsattsauran ra'ayi a kan intanet tare da karkatar da binciken nasu zuwa ga bidiyoyin YouTube da ke warware maganganun jan ra'ayin da masu tsattsauran ra'ayin ke yi.

## JANYEWA DA/KO KAWAR DA TSATTSAURAN RA'AYI

- Samar da matakan da za su taimaka wa masu tsattsauran ra'ayi wajen fita daga ƙungiyoyi masu tsattsauran ra'ayi ta hanyar ƙarfafa dankon zumunci tsakanin iyalan da taimakon su domin samun aiki tare da shiga ƙungiyoyi masu kyawawan ra'ayoyi.
- Gabatar da faɗakarwa da shawarwari a keɓance ga waɗanda suka bar tafarkin tsattsauran ra'ayi tare da fallasa hanyoyin da ƙungiyoyin masu tsattsauran ra'ayi suka bi domin yaudarar mutane tare kuma da tona ire-iren laifuka da suka aikata.
- Watsa shirye-shiryen gidajen rediyo zuwa wurin da ƙungiyoyin masu tsattsauran ra'ayi ke gudanar da lamuransu tare da ba su ƙarfin guiwar ajiye makamansu da sanar da su game da shirye-shiryen gwamnati da suka shafi gyaran hali.
- Samar da shiri domin firsinoni waɗanda aka juya su zuwa masu tsattsauran ra'ayi ko waɗanda aka same su da laifin da ya shafi tarzomar tsattsauran ra'ayi, wanda wannan shiri zai ba su damar sake tunani game da duniya tare da gina zamantakewa mai lumana da mutanen da a da suke tsammani makiyansu ne.
- Taimaka wa masu tsattsauran ra'ayin da suka sauya tunani domin bayyana yadda suka samu rayuwa bayan sun tuba tare da ƙarfafa wa sauran mutane guiwa domin su ma su yi haka.
- Samar da taimako da jagoranci ga waɗanda ke son tuba daga cikin masu tsattsauran ra'ayi da matasan da ke tausaya wa ra'ayoyin masu tsattsauran ra'ayi.

## GYARAN HALI

- Nazartar firsinoni masu laifin tsattsauran ra'ayi dangane da ra'ayoyin da ke ƙarfafa musu guiwa da kuma matakan da suka yi amfani da su wajen nuna cewa suna kan daidai sannan a gabatar musu da shawarwari gabanin a sake su waɗanda za su taimaka musu wajen fahimtar yadda lamurran suke tare da neman mafita a maimakonsu.
- A faɗakar da firsinonin da ake tuhuma ko waɗanda aka kama da laifin ta'addanci da kuma firsinonin da ka iya ɗaukar tsattsauran ra'ayi, domi taimaka musu wajen magance matsaloli da tashe-tashen hankula ta hanyar fara sauya salon rayuwa da guje wa laifi, wanda cikin matakan har da samar da haɗin kai tsakanin firsinoni yayin da suka fito tare da taimaka musu game da ƙalubale da za su fuskanta yayin da suka fito.
- Samar da taimako da suka shafi hanyoyin kwantar da tarzoma ga mayakan da suka dawo daga ƙasahen ƙetare.

## SAKE HAƊAWA

- Taimaka wa tubabbun masu tattsauran ra'ayi domin sud awo cikin al'umma tare da shiga cikin harkar siyasar lumana da gudanar da ayyukan ci gaba a cikin al'umma.
- Aiki hannu-da-hannu da al'ummomi domin kare wulaƙantuwar 'ya'yan mayaƙan da suke ƙasashen ƙetare ko iyalen da suka dawo, wanda hakan na iya haifar da bambanci ko ma ya sa 'ya'yan su bi sahun iyayensu wajen tsattsauran ra'ayi.
- Taimaka wa tubabbun masu tsattsauran ra'ayin da suka dawo gida domin su sake samun ƙimar da suke da ita a da a cikin al'umma ta hanyar tallafa musu domin su zamo masu faɗakarwa game da kauce wa tsattsauran ra'ayi.

Manazarta: Wannan takardar bayani ta yi amfani da misalan shirin shawo kan tsattsauran ra'ayi daga Rumbun Bayanan Impact Europe's Countering Violent Extremism Database, Wanda aka dubo a http://www.impact.itti.com.pl/index#/inspire/search, da na Radicalization Awareness Network's (RAN), Wanda aka samu a https://ec.europa.eu/home-affairs/what-we-do/networks/radicalisation_awareness_network/ran-best-practices/ran-search_en, sannan da na The Future of Countering Violent Extremism: An Analysis of Current Programming in Jordan na Patrick Stahl and Julia Wilton (Center for Global Affairs at New York University).